Jerin Littafan Shi'a Na 3

# Aƙidar

# Taƙiyya

# a wajen

# 'Yan Shi'a

Umar Labɗo

# بسم الله الرحمن الرحيم

Ma'anar Taƙiyya ita ce bayyana saɓanin abinda yake zuci, watau mutum ya faɗi saɓanin abinda ya ƙudure a zuciyarsa, ko ya aikata wani aiki tare da nuna cewa ya yarda da aikin amma a zuciyarsa yana ganin aikin ba dai-dai ba ne, ko bai dace ba, ko kuma haramun ne. Zai yi haka da niyyar jawo hankalin wasu, ko yaudarar su, da nuna musu kansa ba a haƙiƙanin yadda yake ba.

Ayatullahi Khumaini ya bayyana ma'anar taƙiyya a wajen 'yan Shi'a, kamar haka: "Taƙiyya ma'anarta ita ce mutum ya faɗi magana wacce ta saɓawa ainihin abinda yake akwai, ko ya aikata wani aiki wanda yake saɓa wa mizanin Shari'a."[1]

Manufar Taƙiyya ita ce jawo hankalin mutane da samun yardarsu da soyayyarsu ta hanyar ɓoye abinda aka san ba sa so, ko ba zai karɓu ba a wajensu. Khumaini yana faɗi dangane da haka, "An shar'anta Taƙiyya domin yin kara ga mutane da jawo soyayyarsu da ƙaunarsu."[2] A wani wurin kuma ya ce, "Abin nufi da kara shi ne ya zama manufar ita ce haɗa kai da ɗayantaka ta hanyar jawo soyayyar ***masu saɓa mana*** da samun ƙaunarsu."[3] Masu saɓa mana, a maganar tasa, su ne duk waɗada ba 'yan Shi'a ba.

'Yan Shi'a sun san aƙidunsu ba za su taɓa karɓuwa ba ga Musulmi, saboda saɓawarsu ga Alƙur'ani da Sunnah da hankali lafiyayye. Don haka suke ɓoye su, su ɗauki salon yaudara da munafurci, wanda suke kira kara, don yaɗa su da tallata su a tsakanin jama'a. Haka nan, suna ɗaukar son

---

[1] Duba **Kashful Asrai** na Ayatullahi Khumaini, bugun Teheran, 1363, shafi na 147.
[2] Duba littafinsa, **Arrasa'il,** bugun Qum-Iran, mujalladi na 2, shafi na 175.
[3] **Arrasa'il,** mujalladi na 2, shafi na 174.

iyalin gidan Annabi(SAW), Ahalul Baiti, a watsayin wani mayafi da suke lullɓe wannan munafurci nasu da shi.

Taƙiyya tana da muhimmanci sosai, da matsayi mai girma, da falala mai yawa a cikin tafarkin Shi'anci. Dangane da wannan, babban malaminsu, Muhammad binu Ya'aƙub Alkulaini, ya ruwaito daga Imaminsu na biyar Abu Ja'afar, wai ya ce: "Taƙiyya tana daga addinina da addinin iyayena. Kuma babu imani ga wanda bai da taƙiyya."[1]

Babu shakka dangana wannan riwaya ga Abu Ja'afar, Allah ya yi masa rahama, ƙarya ce tsagwaronta; saboda Abu Ja'afar da iyayensa ba su san munafurci ko yaudara ba.

'Yan Shi'a suna amfani da Taƙiyya a matsayin wani mayafi da suke lulluɓe bidi'arsu da miyagun aƙidojinsu da shi. Suna da hanyoyi masu yawa na yin haka. Da farko dai, idan bai zama dole ba, ɗan Shi'a ya kan so ya ɓoye haƙiƙanin cewa shi ɗan Shi'a ne, musamman inda ya san mutane suna da wayewa game da ƙungiyar. Idan kuma asirinsa ya tonu, aka san cewa shi ɗan Shi'a ne, to sai ya yi ƙoƙarin nuna cewa ba wani abu ne Shi'a ba face ƙaunar iyalin gidan Annabi(SAW), watau Ahalul Baiti, da goyon bayan su da jiɓintar su.

Koda yake 'yan Shi'a suna ƙudure matuƙar gaba da ƙiyayya ga Sahabban Annabi, waɗanda suke ɗaukar su a matsayin kafirai da suka yi ridda, amma suna ɓoye wannan ƙiyayya da ƙuduri nasu, ba sa bayyana su ga mutane. Sau da yawa ma su kan yi musun hakan, kuma su kan nuna cewa ƙin Sahabbai wani mummnan abu ne wanda bai kamata a zarge su da shi ba. Amma littafansu da maganganunsu suna tabbatar da haka.

---

[1] Duba **Usulul Kafi** na Muhammad binu Ya'aqub Alkulaini, bugun Darul Murtadi, Bairut, Lebanon, 1426, mujalladi na 2, shafi na 219.

Haka nan, ‘yan Shi’a suna yin taƙiyya dangane da Alƙur’ani mai girma, inda suke nuna cewa su ma suna ban gaskiya da shi kamar sauran Musulmi, duk da yake suna ƙudure cewa wai Sahabbai sun yi sauye-sauye a cikinsa. Ga aƙidar Shi’a, Alƙur’ani an yi ƙari da ragi a cikinsa, saboda haka ba dukkaninsa suka yarda da shi ba. Amma suna ɓoye wannan ƙuduri nasu, su nuna cewa sun yarda da Alƙur’ani dukkaninsa.

Wani salon Taƙiyya kuma da ‘yan Shi’a suke nunawa shi ne makirci a cikin alaƙar su da mutane. Za ka ga ɗan Shi’a yana yin kirki, yana haba-haba da mutane, kuma yana taimakon su, amma duk yana yin haka ne domin jawo hankalinsu da shigar da su tafarkin Shi’anci. A wani yayi, su kan gabatar da taimako da agaji ga marasa lafiya, ko mabukata, da sunan taimakon ‘yan uwa Musulmi, amma duka Taƙiyya ce. Manufarsu a koda yaushe ita ce jawo hankalin mutane waɗanda ba su san haƙiƙanin tafarkinsu ba.

## Fagagen Taƙiyya

Taƙiyya a wajen ‘yan Shi’a tana shiga dukkanin fagage na addini da rayuwa. Suna yin Taƙiyya a cikin ma’amala, kamar yadda muka gabatar, kuma suna yin ta a cikin ibadoji da harkoki na yau-da-kullum.

## Taƙiyya a Cikin Sallah

‘Yan Shi’a suna yin Taƙiyya a cikin sallah, kuma wannan yana ba su dama su yi sallah tare da Ahalus Sunnah domin su yaudare su. Koda yake suna ɗaukar Ahalus Sunnah a matsayin kafirai, saboda ba su yi imani da Imamai ba kuma ba su barranta daga Sahabbai ba, amma yana halatta a gare

su su bi su sallah, kuma sallar ta inganta ba sai sun rama ta ba, matuƙar dai da niyyar Taƙiyya suka yi ta.

Babban malaminsu, Ayatullahi Ruhullahi Khumaini, yana faɗi dangane da kama hannu a sallah kamar haka: "Ɗora ɗayan hannaye a bisa ɗayan, ***kamar yadda masu saɓa mana suke yi***, yana ɓata sallah idan an yi hakan da gan-gan. Amma babu laifi idan aka yi shi a bisa ga Taƙiyya."[1] Masu saɓa mana, yana nufin Ahalus Sunnah.[2]

Magajin Khumaini, watau jagoran ƙasar Iran a yau, Ayatullahi Ali Khamna'i, da aka tambaye shi, ya ce: "Sallah na inganta a bayansu (Ahalus Sunnah) idan ya zama an yi ta saboda kara gare su."[3] Kara, a maganarsa, tana nufin yaudara.

Har yau, an tambayi wani babban malamin nasu mai suna Ayatullahil Uzma Abul Kasim Alkhu'i: Shin sallah na inganta a bayan limami Ahalus Sunna? Sai ya ce, "Tana inganta idan an yi ta bisa Taƙiyya."[4]

Shi kuwa Ayatullahi Muhammad Rida Musawi Kalbayakani cewa ya yi, "Babu laifi a yi sallah a bayansu tare da larura, amma idan ba larura to za'a rama sallar idan an samu ikon yin haka."[5]

Mai karatu zai lura cewa sharaɗin sallar ɗan Shi'a a bayan Ahalus Sunna shi ne Taƙiyya ko larura. Idan larura ta sa shi, to zai rama idan ya samu iko. Amma idan ya yi bisa Taƙiyya ne to sallar ta inganta, kuma ba sai ya rama ba. A wani ƙaulin ma cewa aka yi zai samu lada, kamar yadda ya zo a wata ruwayar daga malaminsu, Kalbayakani, ya ce: "Sallah na inganta a bayan Ahalus Sunna a yayin Taƙiyya, kuma ladan hakan yana da yawa."[6]

---

[1] A duba **Taharirul Wasila** na Khumaini, mujalladi na 1, shafi na 186.
[2] Duba littafinmu **Matsayin Musulmi a Wajen 'Yan Shi'a**.
[3] A duba **Ajwibatul Istifta'at** na Ali Khamna'i, bugun Darul Haqqi, Bairut, shafi na 178.
[4] Duba **Masa'ilun Wa Rudud** na Khu'i, bugun Qum, mujalladi na 1, shafi na 26.
[5] Duba littafinsa, **Irshadus Sa'il**, bugun Maktabatul Faqih, Kuwait, shafi na 39.
[6] Duba **Majma'ul Masa'il** na Kalbayakani, bugun Maktabatul Irfan, Kuwait, mujalladi na 1, shafi na 194.

## Taƙiyya a cikin Azumi da Hajji

Kamar yadda ya halasta ga ɗan Shi'a ya yi Taƙiyya a sallah, haka nan ya halasta gare shi ya yi Taƙiyya a cikin azumi da hajji domin yaudarar Ahalus Sunnah.

Babban malamin Shi'a na wannan zamani, wanda 'yan Shi'ar Nijeriya suke yin koyi da shi, Ayatullahi Khumaini, yana cewa: "A sani abinda ake fa'idanta daga ruwayoyi shi ne ingancin aikin da aka gina a kan Taƙiyya, sawa'un an yi Taƙiyyar ne saboda saɓanin dake tsakaninmu da su (Ahalus Sunna) a hukunci, kamar shafa a kan huffi da buɗa baki da zarar gudan rana ya faɗi, ko kuwa saboda saɓanin tabbatar faruwar wani abu, kamar kamawar wata, misali tsayuwar Arafa a ranar takwas ga wata saboda su a wajensu tara ne."[1]

Abinda Khumaini yake faɗi a nan shi ne, ruwayoyi daga Imaman Shi'a suna tabbatar da cewa duk aikin da aka gina shi a kan Taƙiyya ya inganta. Sai ya ba da misali da cewa, idan ɗan Shi'a ya yi shafa a kan huffi don ya yaudari Ahalus Sunna, ko ya gaggauta buɗa baki, to aikinsa ya inganta duk da cewa su a wajensu waɗan nan abubuwa biyu ba sa inganta.

Kamar yadda aka sani, 'yan Shi'a ba sa shafa a kan huffi (wanda Sunna ce ta Annabi (SAW) amma su ba su yarda da ita ba) kamar yadda ba sa gaggauta buɗa baki (wanda shi ma Sunna ce da suke musun ta) sai dai su jinkirta sai taurari sun fito.[2] Haka nan, idan ɗan Shi'a bai ga wata ba yana iya kama azumi tare da Ahalus Sunna a kan Taƙiyya kuma azumin nasa ya yi, kamar yadda yake iya tsayuwar Arafa ranar takwas ga watan Zul Hijja (a lissafinsa) idan Ahalus Sunna suka ce tara ne, kuma hajjinsa ya yi.

---

[1] A duba littafin **Arrasa'il** na Khumaini, bugun Qum, 1385 B.H., mujalladi na 2, shafi na 196.

[2] Duba littafinmu, **Bacin Tafarkin 'Yan Shi'a,** babin Fikihun 'Yan Shi'a.

Duba ka gani, ya ɗan uwa mai karatu, wannan abin mamaki na ‘yan Shi’a. Su ba abinda ya dame su! Ko ina ta faɗi sha ne a wajensu. Su dai su ɓoye gaskiyar lamarinsu; kada a gane su. Wannan addini na ‘yan Shi’a da arha yake! Anya Allah ake nufi da wannan addinin?!

## Taƙiyya a Jana’iza da Sallar Gawa

‘Yan Shi’a suna yaudarar Ahalus Sunna wajen halartar jana’izar mamatansu da yi musu sallah, amma ba addu’a suke yi musu ba; la’anar su suke yi. Wannan shi ne abinda manyan malamansu, kai har ma da Imamansu (a faɗinsu) suke koya musu.

Wani malami daga cikin magabatansu mai suna Muhammad binu Muhammad binu Nu’uman wanda suke wa laƙabi da Almufid, yana cewa: “Ba ya halasta ga wani daga cikin masu imani ya wanki mai saɓa wa gaskiya dangane da wilaya. Kuma kada ya yi masa sallah sai dai idan larura ta tilasta masa yin haka bisa ga Taƙiyya. To sai ya wanke shi irin wankin masu saɓa mana, kuma kada ya ba shi wasiƙa.[1] Sa’an nan idan ya yi masa sallah, to sai ya la’ance shi, kada ya yi masa addu’a a cikinta.”[2]

Malaman Shi’a sun karɓo ruwaya daga Imaminsu na shida, Abu Abdillah Ja’afar Sadiƙ (Allah ya rahamshe shi kuma ya isar masa ƙarerayin da aka laƙa masa) cewa wai, “Wata rana Hussaini binu Ali (Imami na uku ke nan a wajen ‘yan Shi’a, Allah ya ƙara masa yarda) ya fita zuwa jana’izar wani munafuki da ya mutu, sai ya gamu da wani almajirinsa. Ya tambayi almajirin: Ina za ka, wane? Sai ya ce: Ina guje wa jana’izar wan nan munafukin ne; kada in yi masa sallah. Sai Hussaini ya ce masa: Zo mu je ka

[1] ‘Yan Shi’a suna danka wasika a hannun mamatansu, su bunne su da ita. Wani kaset da suka nuna yadda suke jana’iza a nan Nijeriya ya tabbatar da haka. Nemi kaset din don ka gane wa idanunka.

[2] Duba littafin **Almuqni’ah** na Binu Nu’uman Almufid, bugun Mu’asasatun Nashril Islami, Qum-Iran, shafi na 85.

tsaya a damana, duk abinda ka ji na faɗi ka faɗa. Lokacin da liman ya yi kabbara a kan (mamacin) sai Hussaini ya ce: Allahu Akbar! Ya Allah, ka la'anci wane bawanka la'ana dubu, haɗaɗɗiya ba rababbiya ba. Ya Allah, ka wulaƙanta bawan nan naka a cikin bayi, ka shigar da shi zafin wutarka, ka ɗanɗana masa tsananin azabarka, domin ya kasance yana ***jiɓintar maƙiyanka,*** yana ***gaba da masoyanka,*** yana ƙin iyalin gidan Annabinka."[1]

Jiɓintar maƙiyan Allah, a wajen 'yan Shi'a, shi ne soyayya ga Sahabbai, gaba da masoyan Allah kuma ƙin Ahalul Baiti. Waɗan nan su ne sifofin Ahalus Sunna da malaman Shi'a suke laƙa musu bisa ƙarya da zalunci. Ahalus Sunna suna son, kuma suna jiɓintar, Sahabbai da Ahalul Baiti dukkaninsu, Allah ya ƙara yarda a gare baki ɗaya.

Har yau, Alhurrul Amili ya ruwaito a cikin littafinsa, **Wasa'ilus Shi'a,** daga Abu Abdillahi wai y ace, "Idan (mamacin) mai musun gaskiya ne sai ka ce: Ya Allah, ka cika cikinsa da wuta, ka cika ƙabarinsa da wuta, ka aiko masa da macizai da kunami!"[2]

Ya ɗan uwa mai karatu, dubi wannan ƙiyayya da ƙeta da mugun nufi dake cike da zukatan 'yan Shi'a, kuma suna dangana shi bisa ƙarya ga zaɓaɓɓun bayin Allah, shiyagabannin Ahalul Baitti. Muna roƙon Allah ya shirye su, ya shiryatar da mu baki ɗaya.

## Shin Gaskiya Ne 'Yan Shi'a Suna Son Ahalul Baiti?

Babban makamin Taƙiyya da 'yan Shi'a suke amfani da shi, shi ne son iyalin gidan Annabi(SAW), watau Ahalul Baiti, da jiɓintar su, da goyon bayan su. Amma wannan da'awa tasu, maganganunsu da rubuce-rubucensu

[1] Wannan ruwaya Aldusi ya fitar da ita a cikin littafinsa, **Tahzibul Ahakami,** mujalladi na 3, shafi na 197; da Ibnu Babawaihi Alqummi a cikin **Man La Yahaduruhul Faqih,** mujalladi na 1, shafi na 105; da Alhurrul Amili a cikin **Wasa'ilus Shi'a,** mujalladi na 2, shafi na 771.

[2] Duba **Wasa'ilus Shi'a** na Muhammad binul Hassan Alhurrul Amili, mujalladi na 2, shafi na 771.

suna ƙaryata ta. Za mu kawo misalai na irin waɗan nan maganganu nasu waɗanda muka tsamo daga cikin littafan manyan malamansu.

## Taɓargazarsu Ga Annabi(SAW)

Da farko dai ‘yan Shi’a sun yi wa Annabi(SAW) cin fuska ta hanyar zargin iyalinsa, watau Innar Muminai A’isha(RA), da zina, da nacewarsu a kan wannan zargi duk da kuɓutarwa, da barrantarwa, da wankewa da Alƙur’ani ya yi mata daga wannan zargin. Sa’an nan, suka zargi manyan Sahabbansa, kuma surukansa, da liwaɗi, watau Umar binul Khaɗɗabi uban matarsa Hafsa da Usmanu binu Affan mijin ɗiyansa biyu, Ruƙayya da Ummu Kulthum. Babu shakka a cikin wannan zargi ga waɗanda suke kusa da Annabi, yake son su, kuma ya yarda da su, akwai cin fuska ga Manzo(SAW) da keta irili da suka mummuna.

Amma ‘yan Shi’a ba su tsaya a nan ba. A’a sun fito fili sun faɗi wasu munanan maganganu da suke nuna suka ga Annabi(SAW) kai tsaye. Ba za mu kawo misalai masu yawa ba saboda muninsu, amma za mu ba da misali ɗaya rak saboda mai karatu ya gani da idanunsa irin abinda ‘yan Shi’a suke faɗi a haƙƙin Annabinmu Muhammad(SAW), kuma ya san cewa da’awar son Ahalul Baiti Taƙiyya ce kawai suke yi. Ibnu Taimiya ya hakaito faɗinsu cewa, “A ranar lahira za’a ƙona al’aurar Annabi (SAW), saboda ya auri A’isha.”[1] Wal iyazu billahi!!

Wannan ɗanyar magana, wacce take nuna kafircin mai faɗin ta, ‘yan Shi’a na wannan zamani suna maimaita ta, kamar yadda ya zo a littafin **Kashful Asrari wa Tabri’atil A’immatil Aɗhari** na Sayyid Hussain Almusawi. Ya rubuta cewa, ɗaya daga manyan malaman Shi’a na wannan zamani, mai suna Sayyid Ali Garawi, ya ce: “Lallai Annabi (SAW) babu makawa sai al’aurarsa ta shiga wuta saboda ya auri wasu mata mushirikai.”[2] Yana nufin Aisha da Hafsa, Allah ya ƙara musu yarda.

[1] Duba **Majmu’ul Fatawa** na Ibnu Taimiya, bugun Saudi Arabiya, mujalladi na 28, shafi na 262.

[2] Duba **Kashful Asrari** na Musawi, bugun Darul Iman, Iskandariyya, 2002, shafi na 21-22.

Wannan magana ba ta bukatar wani dogon sharhi. Babu shakka cewa, wanda duk yake ƙudure cewa SILIN GASHI ƊAYA na Annabi(SAW) zai shiga wuta, to wannan KAFIRI ne.

Banda wannan, manyan malaman Shi'a suna zargin Annabi(SAW) da cewa ya gaza isar da aike. Ayatullahi Khumaini yana faɗi a cikin littafinsa **Kashful Asrari** kamar haka, "A bayyane take cewa da Annabi ya isar da saƙo dangane da lamarin Imama gwargwadon yadda Allah ya umarce shi, kuma ya yi ƙoƙarin da ya kamata dangane da lamarin, da dukkan wannan saɓani bai taso ba a ƙasashen Musulmi, kuma da ba'a samu ƙiyayya da yaƙoƙa ba, kuma da ba'a samu saɓani ba a tushen addini da ressansa."[1]

Sai mai hankali ya dubi wannan magana da abinda ta ƙunsa: Khumaini yana nufin Annabi(SAW) bai isar da aike ba kamar yadda Allah ya umarce shi, kuma shi ne sanadin gaba da ƙiyayya da yaƙoƙa tsakanin al'umma. Watau ke nan Annabi(SAW) BA RAHAMA BA NE SHI GA TALIKAI, kamar yadda Allah ya sifanta shi a cikn Alƙur'ani, tunda ya zama sanadin yaƙoƙa da ƙiyayya da gaba a tsakanin al'umma. Wal iyazu billahi!!

Har yau, wani malamin Shi'a na wannan zamanin, mai suna Jabir Agani, yana faɗi dangane da Annabinmu(SAW) kamar haka: "Amincin Allah ya tabbata a gare ka, ya Ma'aikin Allah, **amma ka yi kuskure, kuskure mai girma**(!!) a yayin da ka fita daga duniya ba tare da ka yi wasiya ga kowa ba (dangane da al'amarin Imama). Kai za ka ɗauki alhakin hayaniyar da al'umma ta afka a ciki, da fitintinun da take fama da su. Don me ba ka yi wasiya ba, ya Ma'aikin Allah?!"[2]

Sai mu duba wannan magana da kyau, ya 'yan uwa Musulmi. Akwai kafircin da ya wuce mutum ya ce: ANNABI(SAW) YA YI KUSKURE, KUMA BAI ISAR DA AIKEN ALLAH BA? Wal iyazu billah!!

Wannan ita ce maganar masu da'awar cewa suna son iyalin gidan Annabi(SAW), watau Ahalul Baiti, kuma suna jiɓintar su, suna goyon bayan su!! A bayyane take cewa wannan da'awa Taƙiyya ce kawai.

---

[1] Duba **Kashful Asrari** na Khumaini, shafi na 50.

[2] A duba **Shafin Gizo** mai adireshi kamar haka: http://www.youtube.com/watch?v=l 8s KGuwa 4o.

## Taɓargazarsu Ga Ali(RA)

A cikin ƙoƙarinsu na ɓata sunan shugabannin Musulunci da siffanta su da siffar marasa mutunci, malaman Shi'a suna dangana maganganu masu yawa ga Sarkin Musulmi Ali binu Abi Ɗalib, Allah ya ƙara masa yarda, irin maganganun da ba mai furta su sai wanda ya kai matuƙa a rashin mutunci. Babban malaminsu mai suna Muhammad Baƙir Almajalisi ya ruwaito cewa: Wata mace ta miƙe a cikin masallaci, alhalin Sayyidina Ali yana yin huɗuba, sai ta ce, "Ya kai makashin masoya!" Wai sai Sayyidina Ali ya dube ta, ya ce: "Ya ke mara kunya, ya ballagaza. Ya wacce ba ta haila kamar yadda mata ke haila. **Ya wacce a kan abin naninta akwai wani abu da ya burtso, yana reto."**[1] "ABINNANI," wannan fassarata ce, amma shi mai ruwayar ya yi amfani da wata kalmar Larabci da take nufin FARJI, wacce idan da za mu fassara ta zuwa Hausa to da sai dai mu koma ga tsohuwar Hausa ta Maguzawa mu nemo kalmar.

Saboda Allah, ya ɗan uwa mai karatu, tana yiwuwa Ali binu Abi Ɗalib, Allah ya ƙara masa yarda, ya furta waɗannan kalmomi, alhali yana kan mimbari yana huɗuba a masallaci? Kuma idan ya yi nufin ladabtar da wannan matar ne, ko mayar mata da martani, babu wasu kalmomin da suka fi dacewa da matsayinsa na Sahabi, kuma ƙanin Annabi(SAW), wanda ya taso aka raine shi a gidan Annabta? Babu shakka wannan ƙoƙarin ɓata sunan Ali ne, da ma sauran Ahalul Baiti, da 'yan Shi'a suke yi, kuma a lokaci guda suna fakewa (suna yin Taƙiyya) da cewa wai su masu ƙaunar su ne.

Har yau, akwai wani labari da 'yan Shi'a suke bayarwa cewa, wai wata rana wata mace ta yi wa wani mutum ƙazafi, sai ta ɗauki ruwan ƙwai farin, ta zuba shi a tsakanin ƙafafunta, ta ce wai ya yi lalata da ita, kuma wannan maniyyinsa ne. Wai sai Ali binu Abi Ɗalib(RA) ya tashi, ya duba tsakanin ƙafafunta, ya ce ƙarya take yi, wannan ba maniyyi ba ne!![2]

Mai karatu, sai ka duba wannan magana da idanun basira. Ta ƙaƙa Ali zai duba tsakanin ƙafafun mace muharrama don kawai ya tabbatar da ƙarya ko gaskiyarta?! Shin duka garin ba wata mace wacce za'a sa ta yi wannan

[1] Duba **Biharul Anwari** na Muhammad Baqir Almajalisi, bugun Ihiya'ut Turathi, Bairut, 1403, mujalladi na 41, shafi na 293.

[2] Duba **Biharul Anwari** na Majalisi, mujalladi na 4, shafi na 303.

aikin? Shin wannan ba ƙoƙarin zubar da mutuncin Sarkin Musulmi Ali ba ne?

## Taɓargazarsu Ga Nana Faɗima(RA)

Malaman Shi'a sun siffanta Nana Faɗima, Allah ya ƙara mata yarda, da siffofi waɗanda suke nuna matuƙar suka da zubar da girma. A nan ma, za mu taƙaita saboda munin waɗannan siffofin. A dangane da gadonta da suka ce wai Khalifa Abubakar Siddiƙ ya hana ta, kuma wai Umar ya ɗaure masa gindi a kan haka, suna ruwaito yadda ita Faɗima ɗin ta kai gwauro ta kai mari don neman gadon nata. Suka ce, "Faɗima(AS) ta iske Abubakar da Umar a masallaci, ta yi musu maganar gadonta na gonar Fadak, inda ta yi faɗa da su, ta yi kururuwa, mutane suka taru, kuma ta kama wuyan Umar ta jawo shi zuwa gare ta."[1]

Mai karatu ya dubi yadda wannan ruwaya ta siffanta Faɗima: matar aure, Musulma, ta iske mazaje, abokan ubanta (kuma surukansa), a bainar jama'a, ta yi faɗa da su a kan gona, har ta ci kwalar ɗayansu!! Shin idan ma wannan gadon ya dame ta, ba ta da miji, ko wani ɗan uwa, da zai karɓo mata haƙƙinta? Ai ba Faɗima ba, wacce take Balarabiya, Baƙuraishiya, Bahashima, kuma 'yar Manzon Allah(SAW), ko wata 'yar Fulani Bakanuwa, ba za ta aikata wannan rashin mutuncin ba. Amma abin mamaki shi ne, 'yan Shi'a sun yarda da wannan ruwaya, kuma suna kattaba ta a cikin littafansu!!

Irin waɗan nan maganganu na ɓatanci da 'yan Shi'a suke dangana wa Ahalul Baiti suna da yawa ainun a cikin littafansu. A nan, mun kawo ɗan misali ne kawai don mu tabbatar wa da mai karatu cewa da'awar ƙaunar iyalin gidan Manzon Allah(SAW) da Shi'awa suke yi munafurci ne kawai da yaudara da Taƙiyya!!

[1] Duba **Kitab Salim binu Qais** na Salim binu Qais Alhilali, bugun Mu'assasatul Bi'itha, Bairut, ba tarihi, shafi na 253.